
NOOR
International

# Yana san abin da ke cikin ranka



noor.gallery

بسم الله الرحمن الرحيم

*Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jin qai*




﴿قَدۡ نَعۡلَمُ إِنَّهُۥ لَيَحۡزُنُكَ ٱلَّذِى يَقُولُونَۖ
فَإِنَّهُمۡ لَا يُكَذِّبُونَكَ وَلَٰكِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ
بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ يَجۡحَدُونَ ٣٣﴾

[الأنعام: ٣٣]

Haqiqa Muna da cikakkiyar masaniyar cewa, lalle irin abin da suke faxa yakan baqanta maka rai; to a gaskiya su ba kai suke qaryatawa ba, sai dai azzalumai suna jayayya ne da ayoyin Allah

**Alkur'ani** (6:33)

AIKON DIN AIKI - TONA



NOOR
International

﴿لِيُنفِقۡ ذُو سَعَةٖ مِّن سَعَتِهِۦۖ وَمَن قُدِرَ
عَلَيۡهِ رِزۡقُهُۥ فَلۡيُنفِقۡ مِمَّآ ءَاتَىٰهُ ٱللَّهُۚ لَا
يُكَلِّفُ ٱللَّهُ نَفۡسًا إِلَّا مَآ ءَاتَىٰهَاۚ سَيَجۡعَلُ ٱللَّهُ
بَعۡدَ عُسۡرٖ يُسۡرٗا ٧﴾
[الطَّلَاقِ: ٧]

Mawadaci ya ciyar daidai da wadatarsa; wanda kuwa aka quntata masa arzikinsa, to ya ciyar daidai da abin da Allah Ya ba shi. Allah ba Ya xora wa rai sai gwargwadon abin da Ya ba shi. Kuma da sannu Allah zai sanya sauqi bayan tsanani

**Alkur'ani** (65:7)

AIKON DIN AIKI - TONA



﴿وَلَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ وَنَعۡلَمُ مَا تُوَسۡوِسُ بِهِۦ
نَفۡسُهُۥۖ وَنَحۡنُ أَقۡرَبُ إِلَيۡهِ مِنۡ حَبۡلِ ٱلۡوَرِيدِ ١٦﴾

[ق: ١٦]

Haqiqa kuma Mun halicci mutum, kuma Mun san abin da ransa yake saqa masa; kuma Mu Muka fi kusa da shi fiye da jijiyar wuyansa

**Alkur'ani** (50:16)

AIKON DIN AIKI - TONA



﴿فَبَدَأَ بِأَوۡعِيَتِهِمۡ قَبۡلَ وِعَآءِ أَخِيهِ ثُمَّ ٱسۡتَخۡرَجَهَا مِن
وِعَآءِ أَخِيهِۚ كَذَٰلِكَ كِدۡنَا لِيُوسُفَۖ مَا كَانَ لِيَأۡخُذَ أَخَاهُ فِي
دِينِ ٱلۡمَلِكِ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُۚ نَرۡفَعُ دَرَجَٰتٖ مَّن نَّشَآءُۗ
وَفَوۡقَ كُلِّ ذِي عِلۡمٍ عَلِيمٞ ٧٦﴾

[يوسف: ٧٦]

*Sai ya fara da (binciken) jakunkunansu kafin jakar xan'uwansa; sannan ya fito da shi (mudun) daga jakar xan'uwansa. Kamar haka Muka shirya wa Yusufu; ba zai yiwu ya riqe xan'uwansa ba a shari'ar Sarkin (Masar), sai dai idan Allah Ya ga dama. Muna xaukaka darajojin waxanda Muka ga dama ne. Kuma duk wani mai ilimi akwai wanda yake samansa a ilimi*

**Alkur'ani** (12:76)

AIKON DIN AIKI - TONA




﴿ مَّنِ ٱهۡتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهۡتَدِي لِنَفۡسِهِۦۖ وَمَن ضَلَّ
فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيۡهَاۚ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ أُخۡرَىٰۗ وَمَا كُنَّا
مُعَذِّبِينَ حَتَّىٰ نَبۡعَثَ رَسُولٗا ١٥ ﴾

[الإسراء: ١٥]

Wanda ya shiriya to lalle yana shiriya ne don kansa; wanda kuwa ya vata to lalle yana vata ne don kansa. Ba kuwa wanda zai xauki nauyin laifin wani. Kuma ba Mu zamanto Masu azabtarwa ba har sai Mun aiko da manzo

**Alkur'ani** (17: 15)

AIKON DIN AIKI - TONA




﴿ فَتَعَٰلَى ٱللَّهُ ٱلْمَلِكُ ٱلْحَقُّۗ وَلَا تَعْجَلْ
بِٱلْقُرْءَانِ مِن قَبْلِ أَن يُقْضَىٰٓ إِلَيْكَ وَحْيُهُۥۖ
وَقُل رَّبِّ زِدْنِي عِلْمًا ١١٤ ﴾

[طه: ١١٤]

*Kuma fa Allah Sarki na gaskiya Ya xaukaka (daga maganganun kafirai). Kada kuma ka yi garaje da (karatun) Alqur'ani tun kafin a gama yi maka wahayinsa, kuma ka ce: "Ubangiji Ka qara min ilimi."*

**Alkur'ani** (20: 114)

AIKON DIN AIKI - TONA




﴿ٱلَّذِينَ قَالَ لَهُمُ ٱلنَّاسُ إِنَّ ٱلنَّاسَ قَدۡ جَمَعُواْ لَكُمۡ
فَٱخۡشَوۡهُمۡ فَزَادَهُمۡ إِيمَٰنٗا وَقَالُواْ حَسۡبُنَا ٱللَّهُ وَنِعۡمَ
ٱلۡوَكِيلُ ١٧٣ فَٱنقَلَبُواْ بِنِعۡمَةٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَفَضۡلٖ لَّمۡ يَمۡسَسۡهُمۡ
سُوٓءٞ وَٱتَّبَعُواْ رِضۡوَٰنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ ذُو فَضۡلٍ عَظِيمٍ ١٧٤﴾

[ال عمران: ١٧٣-١٧٤]

*Su ne waxanda mutane suka ce da su: "Lalle mutanen (Makka) fa sun tara muku runduna, to sai ku tsorace su." Amma sai hakan ya qara musu imani, sai suka riqa cewa: "Allah Ya wadace mu, kuma madalla da abin dogara (idan har Shi ne Allah)." (A sakamakon haka) sai suka dawo da ni'ima ta musamman daga Allah da falala, wani abin qi bai shafe su ba, kuma (suka dace da cewa) sun bi yardar Allah. Allah kuma Ma'abocin falala ne wadda take mai girma*

**Alkur'ani** (3: 173-174)

AIKON DIN AIKI - TONA




﴿ ۞ قُلۡ يَٰعِبَادِيَ ٱلَّذِينَ أَسۡرَفُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ لَا
تَقۡنَطُواْ مِن رَّحۡمَةِ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ
جَمِيعًاۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ٥٣ ﴾

[الزمر: ٥٣]

*Ka ce: "Ya ku bayina waxanda suka vata kawunansu sosai (da kafirci da savon Allah), kada ku xebe qauna daga rahamar Allah. Lalle Allah Yana gafarta zunubai baki xaya. Lalle Shi Mai gafara ne, Mai rahama*

**Alkur'ani** (39: 53)

AIKON DIN AIKI - TONA





﴿إِلَّا تَنصُرُوهُ فَقَدْ نَصَرَهُ ٱللَّهُ إِذْ أَخْرَجَهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ثَانِيَ ٱثْنَيْنِ إِذْ
هُمَا فِي ٱلْغَارِ إِذْ يَقُولُ لِصَٰحِبِهِۦ لَا تَحْزَنْ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَنَاۖ فَأَنزَلَ ٱللَّهُ
سَكِينَتَهُۥ عَلَيْهِ وَأَيَّدَهُۥ بِجُنُودٖ لَّمْ تَرَوْهَا وَجَعَلَ كَلِمَةَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
ٱلسُّفْلَىٰۗ وَكَلِمَةُ ٱللَّهِ هِيَ ٱلْعُلْيَاۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ٤٠﴾

[التوبة: ٤٠]

*Idan ba ku taimake shi ba (watau Manzon Allah) to haqiqa Allah Ya taimake shi lokacin da kafirai suka fitar da shi (daga Makka), alhalin suna su biyu, lokacin da suke a cikin kogo, yayin da yake ce wa abokinsa (Abubakar): "Kada ka damu, lalle Allah yana tare da mu," sai Allah Ya saukar masa da nutsuwarsa Ya kuma qarfafe shi da runduna wadda ba ku gan ta ba, Ya kuma sanya kalmar waxanda suka kafirta ta zama qaskantacciya. Kalmar Allah kuwa ita ce maxaukakiya. Allah kuma Mabuwayi ne, Mai hikima*

**Alkur'ani** (9: 40)

AIKON DIN AIKI - TONA




﴿إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّٱلَّذِينَ هُم مُّحۡسِنُونَ ١٢٨﴾

[النحل:١٢٨]

Lalle Allah Yana tare da waxanda suka yi taqawa da kuma waxanda suke masu kyautatawa ne

**Alkur'ani** (16: 128)

AIKON DIN AIKI - TONA


NOOR
International
noor.gallery